*13.* Ashe, kã gani, idan (shi mai hanin) ya ƙaryata, kuma ya jũya bãya?

أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ١٣

*14.* Ashe, bai sani ba cewa Allah Yanã gani?

أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ١٤

*15.* A'aha! Lalle ne idan bai hanu ba, lalle ne zã Mu ja gãshin makwarkwaɗa

كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ١٥

*16.* Makwarkwaɗa maƙaryaciya, mai laifi.

نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ١٦

*17.* Sai ya kirayi ƙungiyarsa.

فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ١٧

*18.* Zã Mu kirayi Zabaniyãwa (mala'iku mãsu girma).

سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ١٨

*19.* A'aha, kada ka bĩ shi. Kuma ka yi tawali'u,(1) kuma ka nemi kusanta (zuwa ga Ubangijinka).

كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ١٩

## SŨRATUL KADR سُورَةُ القَدْرِ

Tana karantar da son Allah ga wannan al'umma ta Musulmi, da Ya ba su Lailatul Kadari dõmin Ya yawaita ladar ayyukansu ko da yake rãyukansu bã su da tsawo kamar na al'ummomin farko.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Lalle ne Mũ, Mun saukar da shi (Alƙur'ãni) a cikin Lailatul Kadari (daren daraja)

إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ فِى لَيْلَةِ ٱلْقَدْرِ ١

(1) Wato salla da sauran ibãdodi.

2. To, me ya sanar da kai abin da ake cewa Lailatul Kadari?

وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ ﴿٢﴾

3. Lailatul Kadari mafi alheri ne daga wasu watanni dubu.

لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ خَيْرٌ مِّنْ أَلْفِ شَهْرٍ ﴿٣﴾

4. Mala'iku da Rũhi suna sauka a cikinsa da iznin Ubangijinsu sabõda kowane umurni.

تَنَزَّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ فِيهَا بِإِذْنِ رَبِّهِم مِّن كُلِّ أَمْرٍ ﴿٤﴾

5. Sallama ne shi daren, har fitar alfijiri.

سَلَٰمٌ هِىَ حَتَّىٰ مَطْلَعِ ٱلْفَجْرِ ﴿٥﴾

## SŨRATUL BAYYINA سُورَةُ البَيِّنَةِ

Tana karantar da hãlãyen kãfirai da mutãnen Littãfi, wãto Yahũdu da Nasãra game da Annabi, tsĩra da amincin Allah su tabbata a gare shi, a gabanin da bayan bayyanarsa.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

1. Waɗanda suka kãfirta daga mũtanen Littafi, da mushirikai, ba su kasance mãsu gushewa daga gaskiya ba har hujja ta je musu.

لَمْ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ تَأْتِيَهُمُ ٱلْبَيِّنَةُ ﴿١﴾

2. Wani Manzo[1] daga Allah, yana karãtun wasu takardu masu tsarki.

رَسُولٌ مِّنَ ٱللَّهِ يَتْلُوا۟ صُحُفًا مُّطَهَّرَةً ﴿٢﴾

(1) Shi ne Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, dõmin bãbu wanda ya dãce da abin da ke cikin littafansu sai shi.